# FADAKARWA

## A kan: Kasuwanci da dabarun sai da kaya

## Kashi na 7a: Sanin abokan cinikinka

### Wanene abokin ciniki?

Abokin ciniki shine mutumin da za a sayarwa da wasu kaya ko za a saya daga gareshi, ko kuma wanda za a yi masa wani aiki ko zai yi aiki. Yana da muhimmanci a san abokan ciniki, sabo da sune kashin bayan kasuwaci.

**Yadda za a gano abokan ciniki masu muhimmanci a gareka:**

- Bincikawa don nemo kungiyoyi masu bukatar kaya.
- Tattaunawa da wadannan kungiyoyi.
- Tattaunawa da sauran yan kasuwa.

**Abokan ciniki sun hada da:**

- Daidaikun manoma, masu noma kayan abinci daban-daban.
- Kungiyoyin manoma, masu noma kayan abinci daban-daban ko, na gari-gari.
- Kananan hukumomi masu sayen kaya domin gwaji wajen wayar da kan jamaʾasu.
- Wasu hukomomin da ba na gwamnati ba, masu gudanar da ayyuka a fannin gona. Misali, hukumomi irin su USAID, Bankin duniya da IFDC suna sayen kaya domin amfani wajen gwaji domin wayar da kan jamaʾa.
- Sauran yan kasuwa wadanda suke da karancin kaya zasu iya saya a wurinka domin biyan bukatun nasu abokan cinikin.
- Sauran jamaʾa wadanda zasu bukaci kaya lokaci lokaci.

**Muhimmin tsokaci akan abokan ciniki:**

- A lura da bukatunsu.
- A lura da karfin aljihunsu.
- A lura da inda suke.
- A jawo hankalinsu.